# Kalmomin sirri

Mahalarta taro za su koyi yanda za su adana bayanansu na intanet cikin ƙarin tsaro ta hanyar yin amfani da kuma kula da kalmomin sirrin masu ƙarfi. Mahalarta taro za su koyi ƙa'idoji a kan tsara kalmar sirri mai ƙarfi, matsalolin raba kalmar sirri. Za su koyi yanda za su adana kalmar sirrinsu cikin tsaro, da kuma yanda za su ɗauki matakin kare shiga cikin asususunsu ba tare da izini ba.

## Kayayyaki darasi

Koyon Abubuwa Game da Takardar Darasi a kan Kalmar Sirri

# Ƙa’idojin Kalmar Sirri

## Kashi Na 1

**Sanar da Ɗalibanka**

Ba ma yin tunani sosai game da kalmomin sirrin da muke yin amfani da su a shafukan yanar gizo, manhajiji, da wasu ayyukan. Duk da haka, yanda kyawon kamomin sirrinka suke shi ke tabbatar da tsaron bayaninka.

**Tattaunawa a Aji**

Sanya mahalarta taron su kasance cikin tattaunawa ta hanyar yin amfani da waɗannan tambayoyin. Ka ɗan tunatar da mahalarta taron cewa yana da muhimmancin kar su raba ainihin kalmomin sirrinsu a lokacin yin wannan aikin ko kuma wasu aikin.

**Tambayi Ɗalibanka**

Kalmomin sirri nawa kake da su?

> Shin kana da kalmomin sirri daban-daban ga kowane asusun imel da dandalin sadarwar zamani?
>
> Shin sun bambanta sosai ko kuma nau’o’i ne na kalmar sirri guda?

Idan kana da kalmar sirri fiye da guda ɗaya, yaya za ka iya tuna ta kowace asusu?

**Tambayi Ɗalibanka**

Kamar a sau nawa ka manta muhimmiyar kalmar sirri?

> Me ka yi a lokacin da ka mance kalmar sirri?
>
> Ta yaya za ka sauƙaƙa tuna kalmar sirrinka?

Shin akwai wata kalmar sirrin da kake yin amfani da ita a kowace rana?

Me zai faru idan — ba tare da saninka ba — wani ya gano kalmar sirrinka?

> Shin zai dogara ne a kan wane ne shi?

Wane irin bayani ne wani zai koya game da kai idan ya yi amfani da kalmar sirrinka

don shiga cikin asusunka?

# Kashi Na 2

**Tattaunawa a Aji**

Shirya maharta taron bibbiyu.

**Sanar da Ɗalibanka**

Tare da abokin aikinka, tattauna abun da zai iya faruwa idan wani wanda ke ƙoƙarin jawo maka matsala ya san kalmar sirrin dandalin sadarwar zamanin da ka fi so.

**Tattaunawa a Aji**

Ba mahalarta taron mintuna 5 domin su tattauna. Nemi ƙungiyoyin da su raba.

**Sanar da Ɗalibanka**

Yi magana da abokin aikinka yanzu game da abun da zai faru idan mai yin kutse ya san kalmar sirrin asusun iyayenka / mai kula da kai.

**Tattaunawa a Aji**

Ba mahalarta taron mintuna 5 domin su tattauna. Sannan, ka nemi ƙungiyoyin da su raba abun da suka tattauna.

# Kashi Na 3

**Sanar da Ɗalibanka**

Za ka iya yin mamaki a kan yanda mai yin kutse zai koyi kalmar sirrin da aka sirrinta. Akwai wasu 'yan hanyoyi; hanya guda ɗya ita ce ta hanyar shawo kan wani — ko yi ma wani wayo domin raba kalmar sirrin shi. Mai yin kutse zai iya yin wannan ta hanyar aikawa da imel da ya yi kama da na ƙwarai wanda ya fito daga dandalin ko shafin yanar gizon da wani ke da asusu. Saƙon imel zai iya neman mutumin ya danna wata kafa sannan ya shiga ciki ta hanyar yin amfani da sunan mai yin amfani da kalmar sirri; a lokacin da mutum ya shiga ciki, mai yin kutsen zai samu wannan bayanin.

Masu yin kutse wasu lokutan suna yin ƙoƙarin yin amfani da fitattun gajerun jimloli kamar "kalmar sirri123," "gwaji" ko kuma sunanka na farko ko sunan ƙarshe.

Wata hanyar da mai yin kutse zai koyi kalmar sirrin da aka sirrinta ita ce ta hanyar abun da ake kira harin "Brute Force." Harin Brute Force yana faruwa ne a lokacin da mai yin kutse ya yi ƙoƙarin shiga asusunka ta hanyar gwaje-gwajen kalmomin sirri da

yawa. A lokacin da mai yin kutse zai iya ƙaddamar da harin “Brute Force” da hannu, An fi yawan yin shi ne ta hanyar gudanar da wani shiri a kwamfuta wanda za ta gwada kowane irin haɗe-haɗen kalmomin sirrin nan take da duk za ka iya tunani. Misali, jerin kalmomin sirrin da ake tunani su ne, ko kuma setin kalmomin sirrin da ke ɗauke da haɗakar baƙaƙe da lambobi daban-daban har sai sun gano lambar da ta yi daidai.

Tabbas, wasu masu kai hare-haren “Brute Force” suna da ƙwarewa. Idan kalmar sirrinka na cikin jerin kalmomin sirrin da ake tsammani, kamar “fido123” ko “kalmar sirri,” washi shirye-shiryen za su iya cinkar ta cikin sauri ta hanyar gwada waɗannan zaɓuɓɓukan kafin waɗanda ba a tsammani ko waɗanda suke barkatai. Harin zai iya zama tsaftatacce idan mai kai harin ya san bayani game da kai. Idan, misali, ya san sunan dabbatka ta gida Toby ne, zai iya gwada ‘Toby’ tare da nau’o’in lambobi daban-daban a ƙarshen kalmar (misali., ‘Toby629,’ ko ‘Toby3020’).

# Tsara Ƙa'idoji

## Kashi Na 1

### Tambayi Ɗalibanka

Wa ya san abun da ake nufi da samun kalmar sirri "mai ƙarfi" ko "ƙarfi"? Me yasa wannan ra'ayin yake da kyau?

### Sanar da Ɗalibanka

Kalmar sirri mai ƙarfi tana taimakawa wajen kare bayananka. Samun kalmar sirri mai ƙarfi ba ya bayar da tabbacin cewa ba za a iya yi ma asusunka kutse ba, samun kalmar sirri mara ƙarfi yana ƙara sauƙaƙa ma wani shiga cikin bayaninka.

## Samar da Horo a kan Kalmar Sirri

### Tambayi Ɗalibanka

Wasu misalai ne na kalmar sirri marasa ƙarfi?

1. Wasu misalan sun haɗa da: Kalmar sirri, 12345, Hello!, kwanan watan hauhuwa, sunan laƙabi.

Me yasa kake ganin waɗannan marasa ƙarfi ne?

1. Wani zai yi saurin cinkarsu/ko wata kwamfutar da ke gudanar da harin "Brute Force".

Wasu hanyoyi ne za ka iya samar da kalmar sirri mai ƙarfi?

1. Ƙara lambobi, manya da ƙananan baƙaƙe, alamomin rubutu, tsawaita kalmar sirri, da kaucewa fitattun gajerun jimloli da kuma kalmomi su kansu.

### Tattaunawa a Aji

Bayan mahalarta taron sun samar da nasu bayanin, rubuta waɗannan umarnin a kan allo:

Haɗa da aƙalla lamba ɗaya.

Haɗa da aƙalla alamar rubutu ɗaya.

Haɗa da aƙalla babban baƙi guda ɗayada ƙaramin baƙi guda ɗaya.

Ya kamata kalmar sirri ta kasance aƙalla baƙaƙe 7.

Ya kamata kalmar sirri ta kasance wadda za a yi sauƙin tunawa (sai dai in za a yi amfani da manajar kalmar sirri).

Manajar kalmar sirri wani shafin yanar gizo ne / manhajar da ke taimakawa masu amfani su adana sannan kuma su tsara kalmar sirrinsu.

Bai kamata kalmar sirri ta kasance kalma ɗaya ba ko bayanin mutun na ƙashin kansa (kwanan watan haihuwa, sunan iyaye, da dai sauransu.).

Bai kamata a raba kalmomin sirri ba a tsakanin shafukan yanar gizo.

**Sanar da Ɗalibanka**

Akwai hanyoyi guda biyu na ƙirƙirar kalmomin sirri masu ƙarfi. Ta farko ita ce bin "tsarin kalmar sirri" kamar wannan da ke kan allon. Yin amfani da tsarin zai ƙarfafa maka guiwa wajen haɗa abubuwan da za su yi wuyar cinka a rubutu/kalmar sirrin mai lamba, sanya kalmar sirrin ta yi wuyar cinka. Matsalar wannan hanyar ita ce tana sa a samu wahala wajen tuna kalmomin sirrin.

## Saita Kalmomin Sirri Masu Ƙarfi

**Sanar da Ɗalibanka**

Wata hanyar ta ƙirƙirar kalmomin sirri masu ƙarfi an danganta ta da tsayin kalmar sirri. Saboda ƙarfin kalmar sirri na da dangantaka da tsayin kalmar sirrin, yin amfani da jerin kalmomi guda huɗu ko fiye waɗanda ba su da dangantaka na sanya kalmomin sirri su yi wuyar cinka ga mutune da kuma harin "Brute Force". Wannan hanyar tana da alfanun da aka ƙara wanda ke haifar da kalmomin sirrin da ke da sauƙin tunawa fiye da hanyar tsara kalmar sirri.

Ta ƙarshe, mutum zai iya haɗa waɗannan hanyoyin guda biyu ta hanyar samar da jerin kalmomi guda huɗu ko fida da ba su da dangantaka, haka kuma a haɗa da alamomin rubutu da kuma lambobi.

Munufar waɗannan hanyoyin mabambanta ɗaya ce: samar da kalmomin sirrin da suke na musamman kuma masu wahalar cinka ga wasu mutanen.

**Sanar da Ɗalibanka**

Shirya maharta taron bibbiyu

Da bibbiyu, gwada ƙirƙirar kalmar sirri mai ƙarfi ta hanyar yin amfani da umarnin da

ka rubuta a kan alla a farko. Ka tuna cewa kalmar sirri da za ta yi ma kwamfuta wahalar cinka na iya yin sauki ga mutane ko kuma wata kwamfutar da ke tare da jerin fitattun kalmomin sirrin da za a cinka. Ba za a kaɓi fallen takardar da ke ɗauke da kalmar sirrinka ba a ƙarshen aikin. Ana ƙarfafa ka cewa kar ka yi amfani da wannan kalmar sirrin ga wani daga cikin asusunka, saboda waɗanda ke cikin ƙungiyar za su iya sani.

Ba mahalarta taron mintuna 5 domin su yi wannan. Ka zagaya ɗakin sannan ka tambayi mahalarta taron abun da suke tunani a kan misalan kalmar sirrinsu mafi ƙarfi. Tambayi mahalarta taron idan za su iya tuna kalmomin sirrin da suka samar ba tare da sun kalle su ba kai tsaye.

Yayin da kuma wasu shafukan yanar gizon za su buƙaci kalmar sirrinka ta cika wsu (ko ma dukkan) waɗannan ƙa'idojin, wasu kuma ba sa ƙayyadewa. Haka kuma za ka iya ƙirƙirar kalmar sirri ta hanyar yin amfani da jerin fitattun kalmomi barkatai.

**Tattaunawa a Aji**

A cikin waɗannan mutum bibbiyun, sanya mahalarta taron su ƙirƙiri sababbin kalmar sirri da suke jirin kalmomi ne. Sanar da su cewa ya kamata ya kasance akwai a ƙalla kalmomin guda huɗu a cikin kalmar sirri don sanyawa su yi ƙarfi da kuma sauƙin tunawa. Ba mahalarta taron mintuna 5 domin su yi wannan. Ka zagaya ɗakin sannan ka tambayi mahalarta taron misalan kalmar sirrinsu. Ka sake, tunatar da mahalarta taron cewa ba za a karɓi fallen takardar ba a ƙarshen aikin, haka kuma ba za a yi amfani da kalmar sirrin ba a cikin asusunsu.

**Sanar da Ɗalibanka**

Wasu shafukan yanar gizon na yin amfani da wani tsari da ake kire mataki-da-yawa (ko mata-biyu) na tantancewa domin tabbatar da kai. Waɗannan shafukan yanar gizon suna yin amfani da saƙwannin kar ta kwana a kai a kai, manhaja, ko imel domin aikawa da wata lamba-ɗaya wadda dole a shigar da ita tare da kalmar sirrin.

Wannan hanyar za ta samarwa asusunka kariya ta hanyar ƙara wani matakin tsaron wanda zai yi wahalar karyawa mataƙa. Misali, domin shiga cikin asusunka, dole ne mutum ya samu kalmar sirrinka da kuma damar shiga manhajar, na'ura, ko adireshin imel wanda aka danganta shi da asusun.

# Adana Kalmar Sirri Cikin Tsaro

## Kashi na Ɗaya

### Sanar da Ɗalibanka

Ko da ka ƙirƙiri kalmar sirrin da za ta yi ma kwamfuta ko wani mutum wahala kutsawa, akwai wasu hanyoyin da kalmar sirri za ta iya yin rauni.

### Tambayi Ɗalibanka

Wasu sauran hanyoyi ne za sanya kalmomin sirrin su yi rauni?

1. Wasu misalan sun haɗa da: sake yin amfani da kalmar sirri ga asusu da yawa, yin amfani da kalmar sirri da ke ɗauke da bayanan sirri, yin amfani da kalmar sirri iri ɗaya a shekaru da yawa, mance kalmar sirrinka.

Kamar a sau nawa ne kake ganin ya kamata ka canza kalmar sirrinka?

### Sanar da Ɗalibanka

Har da kalmomin sirrin masu kyau za a iya yin yarjejeniya ko kuma sacewa, amma akwai abubuwan da za ka iya yi domin ka kare kanka. Idan akwai bayanin da aka kwafa a shafin yanar gizon da kake da asusu, ka tabbata ka canza kalmar sirrinka a kan wannan shafin yanar gizon da duk wasu shafukan yanar gizon da kake da makamantan kalmomin sirri.

Tuna dogaye kalmomin sirri masu yawa da kuma masu rikitarwa zai yi wahala.

### Tambayi Ɗalibanka

Shin kana ganin abu ne mai kyau ka rubuta kalmomin sirrinka a kan fallen takarda, ko kuma a wani daftari a kan kwamfutarka? Mene ne ko kuma me zai hana?

### Tattaunawa a Aji

Ambaci yiwuwar wani zai iya nemo fallen takardar ko kuma ya lura fayil ɗin a kan kwamfutarka. Yi bayani a kan cewa hanya guda ɗaya ita ce ta yin amfani da manajar kalmar sirri, wata manhaja da za ta taimakawa masu yin amfani su adana da kuma tsara kalmar sirrinsu.

## Kashi Na Biyu

### Sanar da Ɗalibanka

Kowace rana, muna yin amfani da amfani da asusu daban-daban da yawa a kan yanar gizo daban-daban. Zai iya yin wahala a shiga ciki sannan a fita daga cikin shafin yanar gizo a kowane lokaci.

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin ka taɓa yin amfani da sigar "adana kalmar sirri" a cikin burauzarka domin adana wata kalmar sirrin shafin yanar gizonka? Mene ne ko kuma me zai hana?

Shin ka fahimci yanda shafin yanar gizo ke tuna kai wane ne?

1. Nemi ƙarin bayani. Sannan ka yi bayanin cewa shafukan yanar gizon za su iya tuna cewa ka shiga ciki ta hanyar adana kuki. Kukis wasu 'yan mitsimitsin fayiloli ne da aka adana a kwamfutarka don taimakawa shafin yanar gizon ya san ka sanan kuma ya san kwamfutarka a ziyarar da za ka kawo a nan gaba, ba tare da sake shiga ciki ba. Duk da haka, za a iya yin amfani da kukis domin a bi sawunka kamar yanda za ka iya tafiya daga shafin yanar gizo zuwa shafin yanar gizo. Wannan ita ce hanyar da tallace-tallace za su cimma ka.

Shin daidai ne a adana kalmar sirri idan a kan taka kwamfutar ne?

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin kwamfutarka tana kalmar sirrin shiga ciki?

Idan fa ka raba kwamfutar da wasu?

1. A wannan halin, ko da za a iya ɓoye kalmar sirrinka a cikin gurbin kalmar sirri ta hanyar ɗige-ɗige baƙaƙe ko alamar taurari, wasu mutanen da ke yin amfani da kwamfutar za su iya gano kalmar sirrinka. Kawai saboda ba za ka iya ganin kalmar sirrinka a allon ba, ba yana nufin cewa ba a adana ta a wani wuri ba.

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin akwai wasu lokutan da suke daidai ne a raba kalmar sirri? Yaushe? Me yasa?

1. Wasu misalan za su iya zama iyaye na son kalmar sirrinsu ko kuma suna da wani asusu na haɗin guiwa/iyali a kan wani sabis kamar Netflix.

Shin ka raba kalmar sirrinka da wani? Idan haka ne, da wa/me yasa?

Idan kuna aminantaka da wasu, za su ce "idan ka damu da ni" kasance wani mai bayar da shawara don ka raba kalmar sirrinka da su? Mene ne ko kuma me zai hana?

**Sanar da Ɗalibanka**

Za ka iya zaɓar ka raba kalmar sirrinka da wani mutum da ka damu da shi, amma kula da su ba yana nufin lallai suna da damar shiga cikin asusunka a intanet ba ne.

Yi tunani a natse game da dangantakar da wani mutumin kafin ka raba, harda wanda ya haɗa da yaya dangantakarku za ta canza a wani lokacin. Misali, rabawa da iyali/mai bayar da kulawa wani zaɓi ne mai bambanci sosi a kan rabawa da amininka.

**Tambayi Ɗalibanka**

Me zai faru da kai idan ka raba kalmar sirrinka?

1. Wani zai iya yi ma asusun bankinka kutse, yi maka zamba ta intanet, ko sanin wasu sirrinka.

Idan ka raba wata kalmar sirri a asusu, shin za ka yi amfani da wannan asusun ta hanya daban?

**Tambayi Ɗalibanka**

Akwai wasu abubuwan da ba ka kalla a Netflix, ko ka rubuta ita hanyar mel idan wani zai iya ganin abun da kake yi?

**Tattaunawa a Aji**

Ya kamata a gani a kan ɗabi'un mahalarta taron a yayin da suke yin amfani da asusun da aka raba. Ya kamata su yi la'akari cewa ayyukansu na intanet za a nuna su ga sauran masu amfanin a kan asusun.

**Tambayi Ɗalibanka**

Idan asusunka na wakiltarka, kamar furofayil ɗin dandalin sadarwar zamani, shin ya yi daidai a ba wasu mutanen damar yin amfani da ausunka?

**Tattaunawa a Aji**

Tattauna yiwuwar wani mutum wanda ke ƙokarin zama kai sannan yake aikewa da saƙonni ga abokanka.

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin kana barin duk wata na'ura da ka yi amfani da ita domin ta adana kalmomin sirrinka? Mene ne ko kuma me zai hana? Shin wannan yana nufin cewa yana da kyau ke nan ka adana kalmomin sirrinka a kan wayarka ta ƙashin kanka ko kuma

kwamfuta? Me zai faru idan ka ba abokinka damar yin burauzin da wayarka ko kwamfutarka?

Shin akwai wata na’urar da ka raba da wasu, kamar iyali ko abokai? Shin ka raba wani asusu a kan wannan na’urar, ko kua shin wani mutum yana da tasu?

Shin ka taɓa yin amfani da na’urar “kowa da kowa” kamar wata a ɗkin karatu a makaranta, ko kuma wani wurin daban? Shin kana yin abu iri ɗaya a kan wannan na’urar da ka yi rin shi a wani wurin?

## Kashi Na Uku

**Tattaunawa a Aji**

Shirya maharta taron bibbiyu.

**Sanar da Ɗalibanka**

A cikin mutune bibbiyunka tattauna ko ka taɓa shiga cikin wata kwamfuta a makaranta, a ɗakin karatu, a cikin wata al’ummar sannan ka ga cewa wani mutum can daban ya shiga cikin sandalin sadar da zumuntarsu ko asusun imel. Nemi da su yi la’aƙari idan za su duba kewayen asusun ko yin wani abun daban.

**Tattaunawa a Aji**

Ba mahalarta taron mintuna 5 domin su tattauna sannan ke nemi su raba. Sanya ƙungiyar a cikin tattaunawa game da yin amfanin da ba a bayar da izini ba.

# Shiga Asusun da Babu Izini

## Kashi na Ɗaya

### Tattaunawa a Aji

Ka lura: An rufe wani ɓangare daga cikin wannan aiken a cikin “Aikin #1: Ƙa’idojin Kalmar Sirri.” Mun jinkirta saboda hukucinka a kan ko dai kana so ka sake duba wannan takardar ko kuma a’a ko kana so ka tsallake ta.

### Sanar da Ɗalibanka

Zai iya yiwuwa wasu mutanen su samu damar shiga asusun, ko da ba su riga sun san kalmar sirrinka ba ko kuma sun yi nasara wajen cinkar kalmar sirrinka. Idan wani ya san isassun bayanan sirri game da kai, za su iya yin wata cinka-cinka cikin ilimi game da kalmar sirrinka, ko kuma ma za su iya shawo kan wani mutum a kamfani domin ya ba su bayananka. Saboda ba sa yin amfani da fasaha wajen shiga asusunka, irin wannan harin ana kiransa kutse cikin bayanan sirri ko shawo kan wani don fallasa bayani.

### Tambayi Ɗalibanka

Ɗaga hannunka idan ka taɓa mance kalmar sirrinka a shafin yanar gizo.

Me zai faru idan ka danna “Na manta kalmar sirrina?

1. Yawanci yafin yanar gizon na tambayar amsoshin tambayoyin tsaro ko kuma ya yi ƙoƙarin haɗa ka ta hanyar yin amfani da lambar waya ko imel.

Wasu tambayoyin tsari ne shafin yanar gizon ke tambaya?

1. Yi bayani a kan tyanda wasu daga cikin waɗannan za su zama tambayoyin da abokai ko abokan hulɗa za su iya amsawa ko cinka. Abubuwa kamar: sunan dabbarsu ta gida, wurin da aka haife su, sunan mahaifin uwa, sunan malamin da suka fi so, sunan amininsu, ƙungiyar wasan da suka fi so.

Wane ne zai iya sanin irin wannan bayanin game da kai?

Yaya shafin yanar gizon ke tuntuɓarka idan ka manta kalmar sirri?

Wane ne kuma zai iya samun damar shiga bayanan tuntuɓarka?

### Tambayi Ɗalibanka

Ta yaya baƙo zai san bayanan sirrin da aka danganta su da amsar tambayoyin tsaronka?

1. Aike a dandalin sadarwar zamani, binciko bayanan mutane a intanet, yin cinka-cinka da yawa, tuntuɓar abokinka. da dai sauransu.

Waɗanne ne misalan aike a dandalin sadarwar zamani masu ɗauke da bayanan sirri?

1. Misali, wani taɗin da a yi a Instagram ɗauke da taken sunan shi, hoton da aka maƙala wuri, yin aiken zagayowar ranar haihuwa a cikin jama'a.

Ta yaya za ka iya yin amfani da Google domin ka ƙara sanin bayanai game da wani da kuma yin kutse a kalmar sirrin shi?

1. Idan na'urar bincike ta nuna maka hoton wani na aji shida a jaridar makaranta a intanet, za ka iya gano sunan malaminsu na aji shidan.

## Kashi Na Biyu

**Sanar da Ɗalibanka**

Aikewa da bayanan da ke ɗauke da amsar tambayar tsaronka zai iya zama babu tsaro. Ka tabbata ka zaɓi tambayoyin tsaron da kai ne kaɗai kake da amsoshin. Haka kuma za ka iya samar da amsoshin tambayoyin tsaro, muddin kana da kana da su a cinin manajar kalmar sirri ko kuma suna da sauƙin tunawa.

Shafukan yanar gizo za su iya tuntuɓar masu yin amfani ta hanyar yin amfani da lamar waya ko adireshin imel ɗin da aka danganta shi da asusun mai yin amfanin. Idan mai yin amfani ya manta da kalmar sirrinsa, shafukan yanar gizon a yawan lokuta suna samar da kalmar sirrin wucin gadi ko wata kafar da mai yin amfani zai iya yin amfani da ita don sake saita kalmar sirrinsa.

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin wannan ita ce hanya mafi kariya da za a tabbatar da cewa mutumin da ke neman sabuwar kalmar sirrin shi ne mai yin amfanin?

Me zai faru idan ka raba adireshin imel ɗin da aka danganta shi da asusun?

1. Hanyar yin amfani da kafa wajen sake saita kalmar sirri ita ce hanya mafi kariya a lokacin, amma idan ka raba asusu ko kalmar sirri da wani mutum daban, za ka iya shiga haɗari.

**Sanar da Ɗalibanka**

Za a iya aiwatar da yin kutsen bayanin sirri daga mutanen da ke tuntuɓarka kai tsaye kuma suke yin ƙoƙarin yi maka wayo wajen ba su bayanai. Wasu lokutan, mutane za su aiko maka da imel suna da'awar cewa wani ne (kamar aboki, iyali ko kuma wani daga banki) sannan su nemi ka bayar da wasu muhimman bayanai (kamar kwanan watan haihuwarka) domin tantance ka. Wanna zai iya zama wata dabara, kamar wani ya yi ma asusun dandalin sadarwar zamanin abokinka kutse sannan ya aiko maka da saƙo (da kuma wasu abubuwan) yana neman kwanan watan haihuwarka ko kuma wurin da ka girma. Idan ka samu wani saƙo daga wurin abokinka wanda ya yi maka bambarakwai, ya kamata ka fara tuntuɓar abokinka (ba a wajen dandalin sadarwar zamani) domin ka tabbatar cewa sune suka aiko maka da saƙon.

Harin da ke yin amfani da imel ɗin da ya yi kama da na ainihi ko shafin yanar gizo ana kiran shi zamba kuma zai iya haifar da zamba cikin aminci. Misali, mai yin zamba cikin aminci zai iya buɗe katin banki da sunanka sannan ya yi amfani da shi, wanda zai iya yi maka wuya ka samu katin banki a lokacin da ka tsufa.

Zamba zai iya ba ɓarawo damar kasancewa kamar kai kuma ya samu damar shiga bayanai da yawa, ba shi damar kutsawa cikin imel ɗinka, aikawa abokanka saƙo yayin da yake ƙoƙarin cewa kai ne, ko kuma ya sace kuɗinka. Haka kuma wannan tsari zai iya ƙyale ɓarawo ya toshe ka daga asusunka ta hanyar ƙirƙirar sabuwar kalmar sirri da ba ka sani ba.

# Aiki

## Takardar darasi

### Aiki

Nemi mahalarta taron da su amsa waɗannan tambayoyin sannan su ƙara da amsoshinsu a matsayin nau'in rubutu ko hotuna ga koyon Game da Takardar Darasi a kan Kalmomin Sirri.

1. Wasu abubuwa ne guda uku da aka fahimta daga cikin wannan sashin da za ka yi amfani da a lokaci na gaba idan za ka ƙirƙiri kalmar sirri?

2. Wane misali ne guda ɗaya na inda kake ganin babu laifi ka raba kalmar sirrinka da wani mutu, daban?

3. Wasu dabaru ne guda uku za ka iya yin amfani da su domin ka raba kalmar sirrinka tare da wani a cikin tsaro?

4. Wasu misalai uku ne na wani abun da zai faru idan kalmar sirrin ta shiga hannun wanda bai kamata ba?

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.